# HADISAI 100

## DOMIN HADDA

LITTAFI NA ƊAYA

**WALLAFAR:**


SASHEN WAYAR DA KAN
AL'UMMA NA ZULFI


**FASSARAR:**


RABIU IBRAHIM YUSUF



1445 - 2024

**Gabatarwa**:

Dukkan godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, Salati da aminci su ƙara tabbata ga mafi ɗaukakar Annabawa da Manzanni, Annabinmu Muhammad ﷺ da iyalan gidansa, da Sahabbansa bakiɗaya, bayan haka.

Wannan littafi ne wanda ya tattara ingantattun hadisan Annabi Muhammad ﷺ, kuma gajeru domin hadda, waɗanda aka fitar da su daga cikin mafiya ingancin litattafai wato Sahihul Bukhari, da Muslim.

Na fassara waɗannan hadisan ne domin fatan shiga cikin waɗanda Annabi ﷺ ya zayyana su a cikin hadisin Abu Hurairah (R.A) haƙiƙa Manzon Allah ﷺ ya ce: “Idan mutum ya rasu aikinsa zai yanke face guda uku: Sadaka mai gudana, ko ilimin da ake amfana da shi, ko ɗa nagari da zai dinga yi masa addu`a”. Muslim ne ya rawaito shi.

Ina fatan Allah Ya sanya ni, tare da ku a cikin waɗanda aikinsu ba zai yanke ba bayan sun rasu.

1. عن أبي هريرة رضي الله عنه عن رسول الله صلى الله عليه وسلم قال: "**كَلِمَتَانِ خَفِيفَتَانِ علَى اللِّسَانِ، ثَقِيلَتَانِ في المِيزَانِ، حَبِيبَتَانِ إلى الرَّحْمَنِ: سُبْحَانَ اللهِ وَبِحَمْدِهِ، سُبْحَانَ اللهِ العَظِيمِ**". متفق عليه.

An karɓo daga Abu Huraira Allah Ya yarda da shi, ya ce: Haƙiƙa Manzon Allah ﷺ ya ce: "(Awai wasu) kalmomi biyu masu sauƙi a kan harshe, masu nauyi a ma'auni, ababen soyuwa a gurin Allah Mairahama: ***(Subhanallahi wa bi hamdihi, subhanal lahil Azim)***, ma'ana: tsarki ya tabbata ga Allah tare da gode masa, tsarki ya tabbata ga Allah mai girma". Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi.

2. عن أبي هريرة رضي الله عنه قال: جَاءَ رَجُلٌ إلى رَسولِ اللَّهِ صَلَّى اللهُ عليه وسلَّمَ فَقالَ: يا رَسولَ اللَّهِ، مَن أحَقُّ النَّاسِ بحُسْنِ صَحَابَتِي؟ قالَ: "**أُمُّكَ**"، قالَ: ثُمَّ مَنْ؟ قالَ: "**أُمُّكَ**"، قالَ: ثُمَّ مَنْ؟ قالَ: "**أُمُّكَ**"، قالَ: ثُمَّ مَنْ؟ قالَ: "**ثُمَّ أبُوكَ**". متفق عليه.

An karɓo daga Abu Huraira Allah Ya yarda da shi, ya ce: “Wani mutum ya zo wajen Manzon Allah ﷺ ya ce: ya Manzon Allah, cikin mutane wa ya yafi cancantar in kyautata zamantakewata da shi? Sai ya ce: (mahaifiyarka), sai ya ce: sai kuma wa? Ya ce masa: (mahaifiyarka), sai ya ce: sai kuma wa? Ya ce: (mahaifiyarka), sai ya ce: sai kuma wa? Ya ce: mahaifinka”. Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi.

3. عن أبي هريرة رضي الله عنه عن النبي صلى الله عليه وسلم قال: "**إِيَّاكُمْ والظَّنَّ، فَإِنَّ الظَّنَّ أَكْذَبُ الحَدِيْثِ**". متفق عليه.

An karɓo daga Abu Huraira Allah Ya yarda da shi, ya ce: Haƙiƙa Annabi ﷺ ya ce: “Ina gargaɗin ku da zato, domin zato shi ne mafi karyar zance”. Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi.

4. عن أبي هريرة رضي الله عنه أَنَّ رسول الله ﷺ قال: "**إنَّ العبدَ لَيتكَلَّمُ بِالكَلِمةِ ما يَتَبَيَّنُ فِيْهَا ، يَزِلُّ بِهَا في النَّارِ أبعدَ مَا بَيْنَ المَشْرِقِ والمَغْرِبِ**". متفق عليه.

An karɓo daga Abu Huraira Allah Ya yarda da shi, ya ce: Annabi ﷺ ya ce: "Haƙiƙa bawa zai ta magana da kalmar da bai yi bincike a kanta ba, wacce za ta tsare shi a wuta sama da nisan gabas da yamma". Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi.

5. عنْ أبي هُريرةَ رَضْيَ اللهُ عَنْهُ عَنَّ النَّبيّ صلَّي اللهُ علَيه وسلَّم، قَالَ: "**إِنَّ اللَّهَ يَغَارُ، وَغَيْرَةُ اللَّهِ أَنْ يَأْتِيَ الْمُؤْمِنُ مَا حَرَّمَ اللَّهُ**". متَّفقٌ عَليْه.

An karɓo daga Abu Huraira Allah Ya yarda da shi, ya ce: Haƙiƙa Annabi ﷺ ya ce: "Allah Yana kishi, kishin Allah shi ne mumini ya je wa abin da Allah Ya haramta" Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi.

6. عن أبي هريرة رَضْيَ اللهُ عَنْهُ أن رسول الله صلى الله عليه وسلم قال: "**مَن قَامَ رَمَضَانَ إيمَانًا واحْتِسَابًا، غُفِرَ له ما تَقَدَّمَ مِن ذَنْبِهِ**". متفق عليه.

An karɓo daga Abu Huraira Allah Ya yarda da shi, ya ce: Haƙiƙa Annabi ﷺ ya ce: "Duk wanda ya tsaya a Ramadana yana mai imani da neman lada za a gafarta masa abin da ya gabata na zunubansa". Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi.

7. عن أبي هريرة رَضْيَ اللهُ عَنْهُ أن رسول الله صلى الله عليه وسلم قال: "**الْعُمْرَةُ إِلَى الْعُمْرَةِ كَفَّارَةٌ لِمَا بَيْنَهُمَا، وَالْحَجُّ الْمَبْرُورُ لَيْسَ لَهُ جَزَاءٌ إِلَّا الْجَنَّةَ**" . مُتَّفَقٌ عَلَيْهِ.

An karɓo daga Abu Huraira Allah Ya yarda da shi, ya ce: Haƙiƙa Annabi ﷺ ya ce: "Umara zuwa umara ana kankare abin da ke tsakaninsu (na zunubai), karɓaɓɓen aikin hajji; ba shi da sakamako sai Aljanna". Bukhari da Muslim ne sika rawaito shi.

8. عَنْ أَبِي هُرَيْرَةَ ـ رضى الله عنه ـ عَنِ النَّبِيِّ صلى الله عليه وسلم قَالَ: **"التَّثَاؤُبُ مِنَ الشَّيْطَانِ، فَإِذَا تَثَاءَبَ أَحَدُكُمْ فَلْيَرُدَّهُ مَا اسْتَطَاعَ"**. مُتَّفَقٌ عَلَيْهِ.

An karɓo daga Abu Huraira Allah Ya yarda da shi, ya ce: Haƙiƙa Annabi ﷺ ya ce: "Hamma daga Sheɗan take, idan ɗayanku zai yi hamma ya yi ƙoƙarin mayar da ita, gwargwadon ikonsa". Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi.

9. أبي هريرة رضى الله عنه ، أن رسول الله صلى الله عليه وسلم قال: **" السَّاعِي علَى الأرْمَلَةِ، والمِسْكِينِ؛ كالْمُجاهِدِ في سَبِيْلِ اللَّهِ، وَأَحْسِبُهُ قَالَ: وَكَالقَائِمِ الّذِيْ لَا يَفْتُرُ، وَكَالصَّائِمِ لَا يُفْطِرُ"**. متفق عليه.

An karɓo daga Abu Huraira Allah Ya yarda da shi, ya ce: Haƙiƙa Annabi ﷺ ya ce: "Mai kaikawo (wajen kulawa da lamarin) bazawara da matalauci kamar mai jihadi saboda Allah yake, ina zaton cewa ya yi: kamar mai tsaiwar da ba ya yankewa yake, kuma kamar mai azumin da ba ya shan ruwa yake". Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi.

10. عن أبي هريرة قال – رضي الله عنه – أن النبي ﷺ قال: **" ما يُصِيبُ الْمُسْلِمَ، مِن نَصَبٍ ولَا وصَبٍ، ولَا هَمٍّ ولَا حُزْنٍ ولَا أذًى ولَا غَمٍّ – حتَّى الشَّوْكَةِ يُشَاكُهَا – إلَّا كَفَّرَ اللَّهُ بهَا مِن خَطَايَاهُ "** .متفق عليه.

An karɓo daga Abu Huraira Allah Ya yarda da shi, ya ce: Haƙiƙa Annabi ﷺ ya ce: " Ba abin da zai sami Musulmi na daga gajiya, ko rashin lafiya, ko zullumi, ko baƙin ciki, ko cuta, ko damuwa, – har ma ƙayar da zai taka – face Allah Ya kankare masa laifukansa da su". Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi.

11. عن أبي هريرة رضي الله عنه، أن رسول الله صلى الله عليه وسلم قال: " **حَقُّ المُسْلِمِ علَى المُسْلِمِ خَمْسٌ :رَدُّ السَّلَامِ، وعِيَادَةُ المَرِيضِ، واتِّبَاعُ الجَنَائِزِ، وإجَابَةُ الدَّعْوَةِ، وتَشْمِيتُ العَاطِسِ"**. متفق عليه.

An karɓo daga Abu Huraira Allah Ya yarda da shi, ya ce: Haƙiƙa Manzon Allah ﷺ ya ce: "Haƙƙin musulmi a kan musulmi biyar ne: Amsa da sallama, da duba mara lafiya, da raka gawa, da amsa gayyata, da gaisar da mai atishawa". Bukhari da Muslim ne suka rawaito.

12. عن أبي هريرة قال: أن رسول الله ﷺ قال: **"مَن شَهِدَ الجَنازَةَ حتَّى يُصَلَّى عليها فَلَهُ قِيراطٌ، ومَن شَهِدَها حتَّى تُدْفَنَ فَلَهُ قِيراطانِ، قيلَ: وما القِيراطانِ؟ قالَ: مِثْلُ الجَبَلَيْنِ العَظِيمَيْنِ"**. متفق عليه.

An karɓo daga Abu Huraira Allah Ya yarda da shi, ya ce: Haƙiƙa Annabi ﷺ ya ce: "Duk wanda ya je jana'iza har aka yi mata salla; yana da ƙiraɗi, wanda kuma ya je har aka binne ta; to yana da ƙiraɗi biyu, sai aka ce: Mane ne ƙiraɗi biyu? Ya ce: Kwatankwacin manyan duwatsu ne guda biyu. Bukhari da Muslim ne suka rawaito.

13. عن أبي هريرة رضي الله عنه قال: **"مَا عَابَ النَّبِيُّ صَلَّى اللَّهُ عَلَيْهِ وَسَلَّمَ طَعَامًا قَطُّ، إِنِ اشْتَهَاهُ أَكَلَهُ، وَإِنْ كَرِهَهُ تَرَكَهُ"**. متفق عليه.

An karɓo daga Abu Huraira Allah Ya yarda da shi, ya ce: "Annabi ﷺ bai taɓa aibanta abinci ba tunda yake, idan ya yi sha'awar shi; sai ya ci shi, idan kuma ba ya son shi; sai ya bar shi". Bukhari da Muslin ne suka rawaito shi.

14. عن أبي هريرة رضي الله عنه أن رسول الله صلى الله عليه وسلم قال : **"حُجِبَتِ النَّارُ بالشَّهَواتِ، وحُجِبَتِ الجَنَّةُ بالمكارِهِ"**. متفق عليه.

An karɓo daga Abu Huraira Allah Ya yarda da shi, ya ce: Haƙiƙa Annabi ﷺ ya ce: "An kewaye wuta da ababen sha'awa, kuma an kewaye aljanna da ababen ƙi". Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi.

15. عن أبي هُريرة رضي الله عنه أن رسول الله صلى الله عليه وسلم قال : **"إِذَا قُلْتَ لِصَاحِبِكَ يومَ الجُمُعَةِ: أنْصِتْ، والإِمَامُ يَخْطُبُ، فقَدْ لَغَوْتَ"**. متفق عليه.

An karɓo daga Abu Huraira Allah Ya yarda da shi: Haƙiƙa Annabi ﷺ ya ce: "Idan ka ce wa abokinka: Yi shiru, a ranar Juma'a, alhalin liman yana huɗuba, to ka yi wargi". Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi.

16. عن أبي هريرة رضي الله عنه قال: أن رسول الله صلى الله عليه وسلم قال : **"لولاَ أن أَشُقَّ عَلَى أُمَّتِي؛ لَأَمَرتُهُم بِالسِّوَاك عِندَ كُلِّ صَلاَة"**. متفق عليه.

An karɓo daga Abu Huraira Allah Ya yarda da shi, ya ce: Haƙiƙa Annabi ﷺ ya ce: "**b**adan kada in takura wa al'umata ba, da na umarce su da yin asuwaki a dukkanin salla". Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi.

17. عن أبي هريرة رضي الله عنه قال: أن رسول الله صلى الله عليه وسلم قال : "**وَيْلٌ لِلأَعْقَابِ مِنَ النَّارِ**. متفق عليه.

An karɓo daga Abu Huraira Allah Ya yarda da shi, ya ce: Haƙiƙa Annabi ﷺ ya ce: "Azaba ta tabbata ga digadigai (waɗanda ba a wanke su a alwala) daga wuta". Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi.

18. عن أبي هريرة رضي الله عنه قال: أن رسول الله صلى الله عليه وسلم قال : "**أَمَّا يَخْشَى الذي يَرْفَعُ رَأْسَهُ قَبْلَ الإمامِ، أنْ يُحَوِّلَ اللَّهُ رَأْسَهُ رَأْسَ حِمارٍ**". متفق عليه.

An karɓo daga Abu Huraira Allah Ya yarda da shi, ya ce: Haƙiƙa Annabi ﷺ ya ce: "Shin wanda ke ɗago kansa (a salla) kafin liman; ba ya tsoron Allah Ya mayar da kansa irin kan jaki?!". Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi.

19. عن أبي هريرة رضي الله عنه أن النبي صلى الله عليه وسلم قال: **"مَنْ غَدَا إلى المسجدِ أو رَاحَ، أَعَدَّ اللهُ له في الجنةِ نُزُلًا كُلَّمَا غَدَا أو رَاحَ"**. متفق عليه.

An karɓo daga Abu Huraira Allah Ya yarda da shi, ya ce: Haƙiƙa Annabi ﷺ ya ce: "Wanda ya yi sammako, ko ya yi yammaci zuwa masallaci, Allah zai tanadar masa da mazaunai a aljanna, a duk lokacin da ya yi sammakon, ko ya yi yammacin". Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi.

20. عن أبي هريرة رضي الله عنه أن النبي صلى الله عليه وسلم قال: **"آيَةُ المُنَافِقِ ثَلاَثٌ: إِذَا حَدَّثَ كَذَبَ، وَإِذَا وَعَدَ أَخْلَفَ، وَإِذَا اؤْتُمِنَ خَانَ"**. متفق عليه.

An karɓo daga Abu Huraira Allah Ya yarda da shi, ya ce: Haƙiƙa Annabi ﷺ ya ce: "Alamomin munafuki guda uku ne: Idan ya yi magana sai ya yi ƙarya, idan ya yi alƙawari sai ya saɓa, idan aka amince da shi; sai ya yi ha'inci". Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi.

21. عن أبي هريرة رضي الله عنه أن النبي صلى الله عليه وسلم قال: **"مَا أَسْفَلَ مِنَ الْكَعْبَيْنِ مِنَ الإِزَارِ فَفِي النَّارِ"**. رواه البخاري.

An karɓo daga Abu Huraira Allah Ya yarda da shi, ya ce: Haƙiƙa Annabi ﷺ ya ce: "Duk abin da ya yi ƙasa da idon sawu na kwarjalle (abin ɗaurawa ko zani na maza); to yana cikin wuta". Bukhari ne ya rawaito shi.

22. عن أبي هريرة رضي الله عنه أن النبي صلى الله عليه وسلم قال: **"المَلاَئِكَةُ تُصَلِّي عَلَى أَحَدِكُمْ مَا دَامَ فِي مُصَلاَّهُ، مَا لَمْ يُحْدِثْ، تقول: اللَّهُمَّ اغْفِرْ لَهُ، اللَّهُمَّ ارْحَمْهُ "**. رواه البخاري.

An karɓo daga Abu Huraira Allah Ya yarda da shi, ya ce: Haƙiƙa Annabi ﷺ ya ce: "Mala'iku suna yin addu'a ga ɗayanku, matuƙar dai yana wajen sallarsa, matuƙar dai bai yi kari ba (wato alwalarsa ba ta karye ba), suna faɗin: Ya Allah Ka yi masa gafara, ya Allah Ka yi masa rahama". Bukhari ne ya rawaito shi.

23. عن أبي هريرة رضي الله عنه أن النبي صلى الله عليه وسلم قال: **"كُلُّ أُمَّتِي يَدْخُلُونَ الجَنَّةَ إِلَّا مَن أَبَى، قالوا: يا رَسُولَ اللَّهِ، وَمَن يَأْبَى؟ قالَ: مَن أَطَاعَنِي دَخَلَ الجَنَّةَ، وَمَن عَصَانِي فقَدْ أَبَى"**. رواه البخاري.

An karɓo daga Abu Huraira Allah Ya yarda da shi, ya ce: Haƙiƙa Annabi ﷺ ya ce: "Dukkanin al'umata za su shiga aljanna, sai wanda ya ƙi", sai suka ce: Ya Manzon Allah waye zai ƙi? Sai ya ce: "Wanda ya yi mini biyayya zai shiga aljanna, wanda ya saɓa mini Haƙiƙa ya ƙi". Bukhari ne ya rawaito shi.

24. عن أبي هريرة رضي الله عنه أن النبي صلى الله عليه وسلم قال: **"إذا قَالَ الرَّجُلُ لأَخِيهِ يَا كَافِرُ، فَقَدْ بَاءَ بِهَا أَحَدُهُمَا"**. رواه البخاري.

An karɓo daga Abu Huraira Allah Ya yarda da shi, ya ce: Haƙiƙa Annabi ﷺ ya ce: "Idan mutum ya ce wa ɗan'uwansa: Kai kafiri, to ɗaya daga cikinsu zai dawo da kalmar (ta kafirci)". Bukhari ne ya rawaito shi.

25. عن أبي هريرة رضي الله عنه أن النبي صلى الله عليه وسلم قال: **"لَلَّهُ أشَدُّ فَرَحًا بتَوْبَةِ أحَدِكُمْ، مِن أحَدِكُمْ بضالَّتِهِ، إذا وجَدَها"**. رواه مسلم.

An karɓo daga Abu Huraira Allah Ya yarda da shi, ya ce: Haƙiƙa Annabi ﷺ ya ce: "Allah ya fi ɗayanku farin ciki da tuban ɗayanku, sama da abin ɗayanku da ya ɓata, idan ya same shi". Muslim ne ya rawaito shi.

26. عن أبي هريرة رضي الله عنه أن النبي صلى الله عليه وسلم قال: **"لاَ تَدْخُلُوا الجْنَّةَ حَتَّى تُؤْمِنُوا، وَلاَ تُؤْمِنُوا حَتَّى تحَابُّوا، أَوَلاَ أَدُلُّكُم عَلَى شَيْءٍ إِذَا فَعَلْتُمُوهُ تحَابَبْتُم، أَفْشُوا السَّلاَمَ بَيْنَكُمْ"**. رواه مسلم.

An karɓo daga Abu Huraira Allah Ya yarda da shi, ya ce: Haƙiƙa Annabi ﷺ ya ce: "Ba za ku shiga aljanna ba har sai kun yi imani, ba za ku yi imani ba har sai kun so juna, shin ba zan nuna muku abin da idan kuka yi shi za ku so juna ba? To ku yaɗa sallama a tsakaninku". Muslim ne ya rawaito shi.

27. عن أبي هريرة رضي الله عنه أن النبي صلى الله عليه وسلم قال: **"الصَّلَوَاتُ الْخَمْسُ وَالْجُمُعَةُ إِلَى الْجُمُعَةِ وَرَمَضَانُ إِلَى رَمَضَانَ، مُكَفِّرَاتٌ لَمَّا بَيْنَهُنَّ، إِذَا اجْتُنِبَتِ الْكَبَائِر"**. رواه مسلم.

An karɓo daga Abu Huraira Allah Ya yarda da shi, ya ce: Haƙiƙa Annabi ﷺ ya ce: "Salloli guda biyar, da Juma'a zuwa Juma'a, da Ramadana zuwa Ramadana, abin kankare abin da ke tsakaninsu ne (na zunubi) idan aka guji manyan zunubai". Muslim ne ya rawaito shi.

28. عن أبي هريرة رضي الله عنه أن النبي صلى الله عليه وسلم قال: **"أَفْضَلُ الصِّيَامِ بَعْدَ رَمَضَانَ شَهْرُ اللَّهِ الْمُحَرَّمِ وَأَفْضَلُ الصَّلَاةِ بَعْدَ الْفَرِيضَةِ صَلَاةُ اللَّيْلِ"**. رواه مسلم.

An karɓo daga Abu Huraira Allah Ya yarda da shi, ya ce: Haƙiƙa Annabi ﷺ ya ce: "Mafificin azumi bayan na Ramadana, shi ne na watan Allah Almuharram, mafificiyar salla bayan ta farilla, ita ce salar dare". Muslim ne ya rawaito shi.

29. عن أبي هريرة رضي الله عنه أن النبي صلى الله عليه وسلم قال: "**مَنْ تَابَ قَبْلَ أَنْ تَطْلُعَ الشَّمْسُ مِنْ مَغْرِبِهَا، تَابَ اللهُ عَلَيْهِ**". رواه مسلم.

An karɓo daga Abu Huraira Allah Ya yarda da shi, ya ce: Haƙiƙa Annabi ﷺ ya ce: "Duk wanda ya tuba kafin rana ta ɓullo daga mafaɗarta, to Allah zai karɓi tubansa" Muslim ne ya rawaito shi.

30. عن أبي هريرة رضي الله عنه أن النبي صلى الله عليه وسلم قال: "**جُزُّوا الشَّوَارِبَ وَأَرْخُوا اللِّحَى، خَالِفُوا الْمَجُوسَ**". رواه مسلم.

An karɓo daga Abu Huraira Allah Ya yarda da shi, ya ce: Haƙiƙa Annabi ﷺ ya ce: "Ku aske gashin baki, ku saki gemu, ku saɓa wa Majusawa". Muslim ne ya rawaito shi.

31. عن أبي هريرة رضي الله عنه أن النبي صلى الله عليه وسلم قال: "**لَأَنْ أَقُولَ (سُبْحَانَ اللَّهِ، وَالْحَمْدُ لِلَّهِ، وَلاَ إِلَهَ إِلاَّ اللَّهُ، وَاللَّهُ أَكْبَرُ)، أَحَبُّ إِلَيَّ مِمَّا طَلَعَتْ عَلَيْهِ الشَّمسُ**". رواه مسلم.

An karɓo daga Abu Huraira Allah Ya yarda da shi, ya ce: Haƙiƙa Annabi ﷺ ya ce: “Wallahi in ce: ***(Subhanallah, wal hamdu lil Lah, wa la ilaha illal Lah, wal lahu Akbar)***, ma’ana: ***(Tsarki ya tabbata ga Allah, godiya ta tabbata ga Allah, babu abin bauta bisa cabcabta sai Allah, Allah Maigirma)***, shi ya fi soyuwa a gare ni, sama da dukkan abin da rana ta ɓullo a kansa”. Muslim ne ya rawaito shi.

32. عن أبي هريرة رضي الله عنه أن النبي صلى الله عليه وسلم قال: **"مَنْ حَمَلَ عَلَيْنَا السِّلَاحَ فَلَيْسَ مِنَّا، ومنْ غشَّنا فليسَ منَّا"**. رواه مسلم.

An karɓo daga Abu Huraira Allah Ya yarda da shi, ya ce: Haƙiƙa Annabi ﷺ ya ce: “Duk wanda ya ɗauki makami a kanmu, ba ya tare da mu, wanda ya yi mana algus ba ya tare da mu”. Muslim ne ya rawaito shi.

33. عن أبي هريرة رضي الله عنه أن النبي صلى الله عليه وسلم قال: "**إِذَا مَاتَ الإِنْسَانُ انْقَطَعَ عنْه عَمَلُهُ إِلَّا مِن ثَلَاثَ: إِلَّا مِن صَدَقَةٍ جَارِيَةٍ، أَوْ عِلْمٍ يُنْتَفَعُ بِهِ، أَوْ وَلَدٍ صَالِحٍ يَدْعُو لَهُ**". رواه مسلم.

An karɓo daga Abu Huraira Allah Ya yarda da shi, ya ce: Haƙiƙa Annabi ﷺ ya ce: “Idan mutum ya mutu aikinsa ya yanke, sai dai guda uku: Sadaka mai gudana, ko ilimin da ake amfanuwa da shi, ko ɗa nagari da zai dinga yi masa addu’a”. Muslim ne ya rawaito shi.

34. عن أبي هريرة رضي الله عنه أن النبي صلى الله عليه وسلم قال: "**لَقِّنُوا مَوْتَاكُمْ: لَا إِلَهَ إِلَّا اللَّهُ**". رواه مسلم.

An karɓo daga Abu Huraira Allah Ya yarda da shi, ya ce: Haƙiƙa Annabi ﷺ ya ce: “Ku laƙanta wa mamatanku: **la’ilaha illallah**”. Muslim ne ya rawaito shi.

35. عن أبي هريرة رضي الله عنه أن النبي صلى الله عليه وسلم قال: " **مَنْ كَذَبَ عَلَيَّ مُتَعَمِّدًا، فَلْيَتَبَوَّأْ مَقْعَدَهُ مِنَ النَّارِ** ". رواه مسلم.

An karɓo daga Abu Huraira Allah Ya yarda da shi, ya ce: Haƙiƙa Annabi ﷺ ya ce: "Wanda ya yi mini ƙarya da gangan; to ya tanadi mazauninsa a wuta". Muslim ne ya rawaito shi.

36. عن أبي هريرة رضي الله عنه أن النبي صلى الله عليه وسلم قال: "**مَن دَعا إلى هُدًى، كانَ له مِنَ الأجْرِ مِثْلُ أُجُورِ مَن تَبِعَهُ، لا يَنْقُصُ ذلكَ مِن أُجُورِهِمْ شيئًا، ومَن دَعا إلى ضَلالَةٍ، كانَ عَلَيْهِ مِنَ الإثْمِ؛ مِثْلُ آثامِ مَن تَبِعَهُ، لا يَنْقُصُ ذلكَ مِن آثامِهِمْ شيئًا**". رواه مسلم.

An karɓo daga Abu Huraira Allah Ya yarda da shi, ya ce: Haƙiƙa Annabi ﷺ ya ce: "Wanda ya yi kira zuwa ga shiriya; to yana da lada irin na wanda ya bi shi, ba za a rage ladansu ba, wanda kuma ya yi kira zuwa ga ɓata; to yana da laifi irin laifin waɗanda suka bi shi, hakan ba zai rage laifinsu da komai ba". Muslim ne ya rawaito shi.

37. عن أبي هريرة رضي الله عنه أن النبي صلى الله عليه وسلم قال: **"قالَ اللَّهُ تَبارَكَ وتَعالَى: أنا أَغْنَى الشُّرَكاءِ عَنِ الشِّرْكِ، مَن عَمِلَ عَمَلًا أشْرَكَ فيه مَعِي غيرِي، تَرَكْتُهُ وشِرْكَهُ"**. رواه مسلم.

An karɓo daga Abu Huraira Allah Ya yarda da shi, ya ce: Haƙiƙa Annabi ﷺ ya ce: "Allah Maɗaukakin Sarki Ya ce: Ni na wadata daga barin masu shirka ga barin shirka, duk wanda ya yi wani aiki ya haɗa ni da wani a cikinsa, to zan kyale shi da shirkarsa". Muslim ne ya rawaito shi.

38. عن أبي هريرة رضي الله عنه أن النبي صلى الله عليه وسلم قال: **" مَنْ صَلَّى عَلَيَّ صَلاةً وَاحِدَةً صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ عَشْرًا "**. رواه مسلم.

An karɓo daga Abu Huraira Allah Ya yarda da shi, ya ce: Haƙiƙa Annabi ﷺ ya ce: "Wanda ya yi mini salati ɗaya, Allah zai yi masa goma". Muslim ne ya rawaito shi.

39. عن أبي هريرة رضي الله عنه أن النبي صلى الله عليه وسلم قال: **"كُلُّ المُسْلِمِ على المُسْلِمِ حَرامٌ؛ دَمُهُ، ومالُهُ، وعِرْضُهُ"**. رواه مسلم.

An karɓo daga Abu Huraira Allah Ya yarda da shi, ya ce: Haƙiƙa Annabi ﷺ ya ce: "Dukkan musulmi a kan musulmi, haramun ne jininsa, da dukiyarsa, da mutuncinsa" Muslim ne ya rawaito shi.

40. عن أبي هريرة رضي الله عنه أن النبي صلى الله عليه وسلم قال: **"مَا نَقَصَتْ صَدَقَةٌ مِنْ مَالٍ، وَمَا زَادَ اللَّهُ عَبْدًا بِعَفْوٍ إِلَّا عِزًّا، وَمَا تَوَاضَعَ أَحَدٌ لِلَّهِ إِلَّا رَفَعَهُ اللَّهُ"**. رواه مسلم.

An karɓo daga Abu Huraira Allah Ya yarda da shi, ya ce: Haƙiƙa Annabi ﷺ ya ce: "Sadaka ba ta tauye dukiya, Allah ba ya ƙara wa bawa wani abu da afuwa face ɗaukaka, ba wanda zai ƙanƙan-da-kai domin Allah; face Allah Ya ɗaukaka shi". Muslim ne ya rawaito shi.

41. عن أبي هريرة رضي الله عنه أن النبي صلى الله عليه وسلم قال: "**أَتَدْرُونَ ما الغِيبَةُ؟** قالوا: اللَّهُ ورَسولُهُ أعْلَمُ، قالَ: **ذِكْرُكَ أخاكَ بما يَكْرَهُ**. قيلَ: أفَرَأَيْتَ إنْ كانَ في أخِي ما أقُولُ؟ قالَ: **إنْ كانَ فيه ما تَقُولُ فَقَدِ اغْتَبْتَهُ، وإنْ لَمْ يَكُنْ فيه فقَدْ بَهَتَّهُ**". رواه مسلم.

An karɓo daga Abu Huraira Allah Ya yarda da shi, ya ce: Haƙiƙa Annabi ﷺ ya ce: “Ko kun san mece ce gulma? ” suka ce: Allah da ManzonSa ne suka sani, ya ce: “Ambatonka ga ɗan’uwanka da abin da yake ƙi” aka ce: To idan kuma akwai abin da nake fadi a tare da dan’uwan nawa fa? Ya ce: “Idan yana da abin da kake faɗi din; to ka yi gulmarsa, idan kuma ba haka ba ne; to ka yi masa ƙage”. Muslim ne ya rawaito shi.

42. عن أبي هريرة رضي الله عنه أن النبي صلى الله عليه وسلم قال: "**سَبَقَ المُفَرِّدُونَ**، قالوا: وَما المُفَرِّدُونَ يا رَسولَ اللهِ؟ قالَ: **الذَّاكِرُونَ اللهَ كَثِيرًا وَالذَّاكِرَاتُ**". رواه مسلم.

An karɓo daga Abu Huraira Allah Ya yarda da shi, ya ce: Haƙiƙa Annabi ﷺ ya ce: “Almutafarridun sun yi rigaye” Sai suka ce: Su waye kuma almutafarridun? Sai ya ce: (Su ne) Masu ambaton Allah da yawa maza da mata”. Muslim ne ya rawaito shi.

43. عن أبي هريرة رضي الله عنه أن النبي صلى الله عليه وسلم قال: **"إِنَّ اللهَ لا يَنْظُرُ إِلى صُوَرِكُمْ، وَأموالِكُم، وَلَكِنْ يَنْظُرُ إِلَى قُلُوبِكُمْ وأعْمَالِكُمْ"**. رواه مسلم.

An karɓo daga Abu Huraira Allah Ya yarda da shi, ya ce: Haƙiƙa Annabi ﷺ ya ce: "Allah ba Ya duban surorinku, ko dukiyoyinku, sai dai Yana duban zukatanku da ayyukanku". Muslim ne ya rawaito shi.

44. عن أبي هريرة رضي الله عنه أن النبي صلى الله عليه وسلم قال: **"لَا تَجْعَلُوا بُيُوتَكُمْ مَقابِرَ، إنَّ الشَّيْطانَ يَنْفِرُ مِنَ البَيْتِ الذي تُقْرَأُ فيه سُورَةُ البَقَرَةِ"**. رواه مسلم.

An karɓo daga Abu Huraira Allah Ya yarda da shi, ya ce: Haƙiƙa Annabi ﷺ ya ce: "Kar ku sanya gidajenku su zama maƙabartu, Sheɗan yana guduwa daga gidan da ake karanta Suratul Baƙara a cikinsa". Muslim ne ya rawaito shi.

45. عن أبي هريرة رضي الله عنه أن النبي صلى الله عليه وسلم قال: **"لا يَدْخُلُ الجَنَّةَ مَن لا يَأْمَنُ جارُهُ بَوائِقَهُ"**. رواه مسلم.

An karɓo daga Abu Huraira Allah Ya yarda da shi, ya ce: Haƙiƙa Annabi ﷺ ya ce: “Wanda maƙocinsa bai aminta daga sharrinsa ba; to ba zai shiga aljanna ba”. Muslim ne ya rawaito shi.

46. عن أبي هريرة رضي الله عنه أن النبي صلى الله عليه وسلم قال: **"أقربُ مَا يَكونُ العبْدُ مِن ربِّهِ وَهَو ساجدٌ، فَأَكثِرُوا الدُّعاءَ"**. رواه مسلم.

An karɓo daga Abu Huraira Allah Ya yarda da shi, ya ce: Haƙiƙa Annabi ﷺ ya ce: “Mafi kusancin lokacin da bawa yake fin kusa da Allah; shi ne sadda yake sujjada, ku yawaita addu’a”. Muslim ne ya rawaito shi.

47. عن أبي هريرة رضي الله عنه أن النبي صلى الله عليه وسلم قال: **"وَمَن سَلَكَ طَرِيقًا يَلْتَمِسُ فيه عِلْمًا، سَهَّلَ اللَّهُ له به طَرِيقًا إلى الجَنَّةِ"**. رواه مسلم.

An karɓo daga Abu Huraira Allah Ya yarda da shi, ya ce: Haƙiƙa Annabi ﷺ ya ce: "Duk wanda ya kama hanya da yake neman ilimi a cikinta, to Allah zai sauƙaƙa masa hanya zuwa aljanna da ita". Muslim ne ya rawaito shi.

48. عن أبي هريرة رضي الله عنه أن النبي صلى الله عليه وسلم قال: **"إِنَّ اللَّهَ يَقُولُ يَوْمَ الْقِيَامَةِ: أَيْنَ الْمُتَحَابُّونَ بجَلَالِي؟ الْيَوْمَ أُظِلُّهُمْ فِي ظِلِّي، يَوْمَ لَا ظِلَّ إِلَّا ظِلِّي"**. رواه مسلم.

An karɓo daga Abu Huraira Allah Ya yarda da shi, ya ce: Haƙiƙa Annabi ﷺ ya ce: "A ranar ƙiyama Allah zai ce: Ina masu son juna saboda girmaNa, a yau zan sanya su a inuwata, ranar da babu inuwa sai tawa". Muslim ne ya rawaito shi.

49. عن أبي هريرة رضي الله عنه أن النبي صلى الله عليه وسلم قال: "**إِذَا أُقِيمَتِ الصَّلَاةُ فَلَا صَلَاةَ إِلَّا الْمَكْتُوبَةَ**". رواه مسلم.

An karɓo daga Abu Huraira Allah Ya yarda da shi, ya ce: Haƙiƙa Annabi ﷺ ya ce: "Idan aka tayar da salla; to ba sauran wata salla sai ta farilla". Muslim ne ya rawaito shi.

50. عن أبي هريرة رضي الله عنه أن النبي صلى الله عليه وسلم قال: "**الدُّنْيَا سِجْنُ الْمُؤْمِنِ وَجَنَّةُ الْكَافِرِ**". رواه مسلم.

An karɓo daga Abu Huraira Allah Ya yarda da shi, ya ce: Haƙiƙa Annabi ﷺ ya ce: "Duniya kurkukun mumini ce, kuma aljannar kafiri ce". Muslim ne ya rawaito shi.

51. عن عائشة رضي الله عنها، عن النبي صلى الله عليه وسلم قال: "**مَنْ أَحْدَثَ فِي أَمْرِنَا هَذَا مَا لَيْسَ مِنْهُ فَهُوَ رَدٌّ**". متفق عليه.

An karɓo daga A'isha Allah Ya yarda da ita, daga Annabi ﷺ ya ce: "Wanda ya farar da wani abu a wannan lamarin (addinin) namu, wanda ba ya daga cikinsa; to abin mayarwa ne (ba za a karɓa ba)". Bukhari, da Muslim ne suka rawaito shi.

52. عن عائشة رضي الله عنها، عن النبي صلى الله عليه وسلم قال: **"أحَبَّ الأعْمالِ إلى اللَّهِ أدْوَمُها وإنْ قَلَّ"**. متفق عليه

An karɓo daga A'isha Allah Ya yarda da ita, daga Annabi ﷺ ya ce: "Mafi soyuwar ayyuka a wajen Allah Maɗaukakin Sarki, su ne waɗanda aka dawwama (ana yi) ko da sun ƙaranta". Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi.

53. عن عائشة رضي الله عنها، عن النبي صلى الله عليه وسلم قال: **"مَنْ نَذَرَ أَنْ يُطِيعَ اللَّهَ فَلْيُطِعْهُ، وَمَنْ نَذَرَ أَنْ يَعْصِيَهُ فَلَا يَعْصِهِ"**. رواه البخاري.

An karɓo daga A'isha Allah Ya yarda da ita, daga Annabi ﷺ ya ce: "Duk wanda ya yi bakance zai yi wa Allah biyayya; to ya yi masa biyayya, wanda kuma ya yi bakancen zai saɓa masa to kada ya saɓa masa". Bukhari ne ya rawaito shi.

54. عن عائشة رضي الله عنها، عن النبي صلى الله عليه وسلم قال: **"لا تَسُبُّوا الأَمْوَاتَ، فَإِنَّهُمْ قَدْ أفْضَوْا إِلَى مَا قَدَّمُوا"**. رواه البخاري.

An karɓo daga A'isha Allah Ya yarda da ita, daga Annabi ﷺ ya ce: "Kada ku zagi matattu, domin sun je wa abin da suka gabatar". Bukhari ne ya rawaito shi.

55. عن عائشة رضي الله عنها، عن النبي صلى الله عليه وسلم قال: **"كان النَّبِيُّ صلّى اللهُ عليه وسلّم لا يَدَعُ أرْبَعًا قَبْلَ الظُّهْرِ، ورَكْعَتَيْنِ قَبْلَ الغَدَاةِ"**. رواه البخاري.

An karɓo daga A'isha Allah Ya yarda da ita, ta ce: "Annabi ﷺ ya kasance ba ya barin raka'a huɗu kafin sallar Azahar, da raka'a biyu kafin sallar Asuba". Bukhari ne ya rawaito shi.

56. عن عائشة رضي الله عنها، قالت: **"كانَ النبيُّ صَلَّى اللهُ عليه وسلَّمَ يُحِبُّ التَّيَمُّنَ ما اسْتَطَاعَ، في شَأْنِهِ كُلِّهِ، في طُهُورِهِ وتَرَجُّلِهِ وتَنَعُّلِهِ"**. رواه البخاري.

An karɓo daga A'isha Allah Ya yarda da ita ta ce: "Annabi ﷺ ya kasance yana son damaitawa (Yin abu da hannun dama) matuƙar iyawarsa, a dukkan lamuransa, a tsarkinsa (alwalarsa), da taje kansa, da sanya takalminsa". Bukhari ne ya rawaito shi.

57. عن عائشة رضي الله عنها، قالت: **"كانَ النبيُّ صَلَّى اللهُ عليه وسلَّمَ يَذْكُرُ اللَّهَ علَى كُلِّ أحْيَانِهِ"**. رواه مسلم.

An karɓo daga A'isha Allah Ya yarda da ita, ta ce: "Annabi ﷺ ya kasance ya na ambaton Allah a dukkan lokutansa". Muslim ne ya rawaito shi.

58. عن عائشة رضي الله عنها، عن النبي صلى الله عليه وسلم قال:"**رَكْعَتَا اَلْفَجْرِ خَيْرٌ مِنْ اَلدُّنْيَا وَمَا فِيهَا**". رواه مسلم.

An karɓo daga A'isha Allah Ya yarda da ita, daga Annabi ﷺ ya ce: "Raka'o'i biyu ta Alijir sun fi duniya da abin da ke cikinta alheri". Muslim ne ya rawaito shi.

59. عن عائشة رضي الله عنها، عن النبي صلى الله عليه وسلم قال: "**إِنَّ الرِّفْقَ لاَ يَكُونُ فِي شَيْءٍ إِلاَّ زَانَهُ وَلاَ يُنْزَعُ مِنْ شَيْءٍ إِلاَّ شَانَهُ**". رواه مسلم.

An karɓo daga A'isha Allah Ya yarda da ita, daga Annabi ﷺ ya ce: "Tausasawa ba za ta shiga wani abu ba; face ta ƙawata shi, ba kuma za a cire ta daga wani abu ba; face ta ɓata shi". Muslim ne ya rawaito shi.

60. عن أنس رضي الله عنه، عن النبي صلى الله عليه وسلم قال: **"لاَ يُؤْمِنُ أَحَدُكُمْ حَتَّى يُحِبَّ لأَخِيهِ مَا يُحِبُّ لِنَفْسِهِ"**. متفق عليه

An karɓo daga Anas ɗan Malik Allah Ya yarda da shi, daga Annabi ﷺ ya ce: "Ɗayanku ba zai yi imani ba; har sai ya so wa ɗan'uwansa irin abin da yake so wa kansa". Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi.

61. عن أنس رضي الله عنه، عن النبي صلى الله عليه وسلم قال: **"مَا مِنْ مُسْلِمٍ يَغْرِسُ غَرْسًا، أَوْ يَزْرَعُ زَرْعًا، فَيَأْكُلُ مِنْهُ طَيْرٌ، أَوْ إِنْسَانٌ أَوْ بَهِيمَةٌ، إِلَّا كَانَت لَهُ بِهِ صَدَقَةٌ"**.

An karɓo daga Anas ɗan Malik Allah Ya yarda da shi, daga Annabi ﷺ ya ce: "Ba wani musulmi da zai dasa wani abin dashe, ko ya shuka wata shuka, sai wani tsuntsu ya ci, ko wani mutum, ko dabba (su ci) face ya zama sadaka a gare shi". Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi.

62.  عن أنس رضي الله عنه، عن النبي صلى الله عليه وسلم قال: **"مَنْ أَحَبَّ أَنْ يُبْسَطَ لَهِ فِي رِزْقِهِ، وَأَنْ يُنْسَأَ لَهُ فِي أَثَرِهِ، فَلْيَصِلْ رَحِمَهُ"**. متفق عليه.

An karɓo daga Anas ɗan Malik Allah Ya yarda da shi, daga Annabi ﷺ ya ce: "Wanda yake so a faɗaɗa masa arziƙinsa, a tsawaita masa bayansa, to ya sa da zumuncinsa". Bukhari da musim ne suka rawaito shi.

63.  عن أنس رضي الله عنه قال: كان النبي صلى الله عليه وسلم يقول: "﴿**رَبَّنَا آتِنَا فِي الدُّنْيَا حسَنَةً وفِي الآخِرَةِ حسَنةً وقِنَا عذَابَ النَّارِ**﴾". متفق عليه.

An karɓo daga Anas ɗan Malik Allah Ya yarda da shi ya ce: Annabi ﷺ ya kasance ya na faɗin: "***Rabbana atina fid dunya hasanatan, wa fil akhirati hasanatan, waƙina azaban nar***" ma'ana: Ya Allah Ka ba mu mai kyau a duniya, a lahira ma Ka ba mu kyakkyawa, Ka kare mu daga azabar wuta". Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi.

64.   عن أنس رضي الله عنه، عن النبي صلى الله عليه وسلم قال: "**إِنَّمَا الصَّبْرُ عِنْدَ الصَّدْمَةِ الأُولَى**". متفق عليه.

An karɓo daga Anas ɗan Malik Allah Ya yarda da shi, daga Annabi ﷺ ya ce: "Kaɗai (ladan) haƙuri na tabbata ne a yayin bugun farko". Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi.

65.   عن أنس رضي الله عنه، عن النبي صلى الله عليه وسلم قال: "**يَتْبَعُ الْمَيِّتَ ثَلاَثَةٌ، فَيَرْجِعُ اثْنَانِ وَيَبْقَى مَعَهُ وَاحِدٌ، يَتْبَعُهُ أَهْلُهُ وَمَالُهُ وَعَمَلُهُ، فَيَرْجِعُ أَهْلُهُ وَمَالُهُ، وَيَبْقَى عَمَلُهُ**". متفق عليه.

An karɓo daga Anas ɗan Malik Allah Ya yarda da shi, daga Annabi ﷺ ya ce: "Abubuwa uku ne suke bin mamaci, sai biyu su dawo ɗaya kuma ya zauna tare da shi, iyalansa, da dukiyarsa, da aikinsa, sai iyalansa, da dukiyarsa su dawo, sai aikinsa ya tsaya (tare da shi". Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi.

66. عن أنس رضي الله عنه، عن النبي صلى الله عليه وسلم قال: **"يَسِّرُوا وَلاَ تُعَسِّرُوا، وَبَشِّرُوا وَلاَ تُنَفِّرُوا"**. متفق عليه.

An karɓo daga Anas ɗan Malik Allah Ya yarda da shi, daga Annabi ﷺ ya ce: "Ku sauƙaƙa kada ku ƙuntata, ku yi bushara kada ku kore jama'a". Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi.

67. عن أنس رضي الله عنه، عن النبي صلى الله عليه وسلم قال: **" سَوُّوا صُفُوفَكُمْ فَإِنَّ تَسْوِيَةَ الصُّفُوفِ من إِقَامَةَ الصَّلَاة "**. متفق عليه.

An karɓo daga Anas ɗan Malik Allah Ya yarda da shi, daga Annabi ﷺ ya ce: "Ku daidaita sahunku, domin daidaita sahu yana daga cikin tsayar da salla". Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi.

68. عن أنس رضي الله عنه، عن النبي صلى الله عليه وسلم قال: "**إِنَّ اللَّهَ لَيَرْضَى عَنِ العَبْدِ أَنْ يَأْكُلَ الأَكْلَةَ فَيَحْمَدَهُ عَلَيْهَا، أَوْ يَشْرَبَ الشَّرْبَةَ فَيَحْمَدَهُ عَلَيْهَا**". متفق عليه.

An karɓo daga Anas ɗan Malik Allah Ya yarda da shi, daga Annabi ﷺ ya ce: “Allah Yana yarda da bawan da zai ci wani abinci sannan ya gode masa a kansa, ko ya sha wani abin sha ya kuma gode masa a kansa”. Muslim ne ya rawaito shi.

69. عن أنس رضي الله عنه، عن النبي صلى الله عليه وسلم قال: "**لَا يُؤْمِنُ أَحَدُكُمْ، حتَّى أَكُونَ أَحَبَّ إِلَيْهِ مِن والِدِهِ ووَلَدِهِ والنَّاسِ أَجْمَعِينَ**". متفق عليه.

An karɓo daga Anas ɗan Malik Allah Ya yarda da shi, daga Annabi ﷺ ya ce: “Ɗayanku ba zai yi imani ba, har sai na fi soyuwa a ransa sama da mahaifinsa, da ɗansa, da dukkanin mutane”. Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi.

70. عن ابن عمر رضي الله عنهما قال: قال رسول الله صلى الله عليه وسلم: **" ما زالَ جِبْرِيلُ يُوصِينِي بالجارِ، حتَّى ظَنَنْتُ أنَّه سَيُوَرِّثُهُ"**. متفق عليه.

An karɓo daga Ibnu Umar Allah Ya yarda da su, ya ce: Annabi ﷺ ya ce: "Mala'ika Jibrilu bai gushe ba ya na yi mini wasiyya da maƙoci, har sai da na yi zaton cewa zai ci gadonsa". Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi.

71. عن ابن عمر رضي الله عنهما قال: قال رسول الله صلى الله عليه وسلم: **"اجْعَلُوا آخِرَ صَلَاتِكُمْ بِاللَّيْلِ وِتْرًا"**. متفق عليه.

An karɓo daga Ibnu Umar Allah Ya yarda da su, ya ce: Annabi ﷺ ya ce: "Ku sanya ƙarshen sallarku da daddare ya zamanto wutiri". Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi.

72. عن ابن عمر رضي الله عنهما قال: قال رسول الله صلى الله عليه وسلم: **"مَا زَالَ الرَّجُلُ يَسْأَلُ النَّاسَ حَتَّى يَأْتِيَ يَوْمَ الْقِيَامَةِ لَيْسَ فِي وَجْهِهِ مُزْعَةُ لَحْمٍ"**. متفق عليه.

An karɓo daga Ibnu Umar Allah Ya yarda da su, ya ce: Annabi ﷺ ya ce: "Mutum ba zai gushe ba ya na rokon mutane, har sai ya zo a ranar ƙiyama babu tsokar nama a fuskarsa". Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi.

73. عن ابن عمر رضي الله عنهما قال: قال رسول الله صلى الله عليه وسلم:**" الَّذِي تَفُوتُهُ صَلَاةُ العَصْرِ فَكَأَنَّمَا وُتِرَ أَهْلَهُ وَمَالَه"**. متفق عليه.

An karɓo daga Ibnu Umar Allah Ya yarda da su, ya ce: Annabi ﷺ ya ce: "Wanda sallar La'asar ta wuce shi, kamar an halakar da iyalansa, da dukiyarsa ne". Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi.

74. عن ابن عمر رضي الله عنهما قال: قال رسول الله صلى الله عليه وسلم: "**الْمُسْلِمُ أَخُو الْمُسْلِمِ لاَ يَظْلِمُهُ وَلاَ يُسْلِمُهُ، وَمَنْ كَانَ فِي حَاجَةِ أَخِيهِ كَانَ اللَّهُ فِي حَاجَتِهِ، وَمَنْ فَرَّجَ عَنْ مُسْلِمٍ كُرْبَةً، فَرَّجَ اللَّهُ عَنْهُ كُرْبَةً مِنْ كُرُبَاتِ يَوْمِ الْقِيَامَةِ، وَمَنْ سَتَرَ مُسْلِمًا سَتَرَهُ اللَّهُ يَوْمَ الْقِيَامَةِ**". متفق عليه.

An karɓo daga Ibnu Umar Allah Ya yarda da su, ya ce: Annabi ﷺ ya ce: "Musulmi ɗan'uwan musulmi ne, kada ya zalunce shi, kada ya miƙa shi (ga abokan gaba), duk wanda ya tsaya a kan (ginin ya biya) buƙatar ɗan'uwansa; to Allah zai tsaya a kan (biyan masa) buƙatarsa, wanda ya yaye wa ɗan'uwansa baƙin ciki; to Allah zai yaye masa baƙin ciki daga cikin baƙƙan cikin ranar ƙiyama, wanda ya suturta musulmi; Allah zai suturta shi a ranar ƙiyama". Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi.

75. عن ابن عمر رضي الله عنهما قال: قال رسول الله صلى الله عليه وسلم: **"كُنْ فِي الدُّنْيَا كَأَنَّكَ غَرِيبٌ أَوْ عَابِرُ سَبِيلٍ"**. رواه البخاري.

An karɓo daga Ibnu Umar Allah Ya yarda da su, ya ce: "Ka kasance a duniya tamkar baƙo, ko mai ƙetare hanya". Bukhari ne ya rawaito shi.

76. عن ابن عمر رضي الله عنهما قال: قال رسول الله صلى الله عليه وسلم: **"الظُّلْمُ ظُلُمَاتٌ يَومَ القِيَامَةِ"**. رواه البخاري.

An karɓo daga Ibnu Umar Allah Ya yarda da su, ya ce: Annabi ﷺ ya ce: "Zalunci duhu ne a ranar kiyama". Bukhari ne ya rawaito shi.

77. عن ابن عمر رضي الله عنهما قال: قال رسول الله صلى الله عليه وسلم: "**الْمُسْلِمُ مَن سَلِمَ الْمُسْلِمُونَ مِن لِسَانِهِ ويَدِهِ، والْمُهَاجِرُ مَن هَجَرَ ما نَهَى اللَّهُ عَنْهُ**". رواه البخاري.

An karɓo daga Ibnu Umar Allah Ya yarda da su, ya ce: Annabi ﷺ ya ce: "Musulmi shi ne wanda musulmai suka kuɓuta daga harshensa, da hannunsa, mai hijira shi ne wanda ya ƙaurace wa abin da Allah Ya haramta". Bukhari ne ya rawaito shi.

78. عن ابن عمر رضي الله عنهما قال: قال رسول الله صلى الله عليه وسلم: "**كُلُّ مُسْكِرٍ خَمْرٌ، وكُلُّ خَمْرٍ حَرامٌ**". رواه مسلم.

An karɓo daga Ibnu Umar Allah Ya yarda da su, ya ce: Annabi ﷺ ya ce: "Duk abin dake bugarwa giya ne, duk abin da ya yake bugarwa haramun ne". Muslim ne ya rawaito shi.

79. عن ابن عمر رضي الله عنهما قال: قال رسول الله صلى الله عليه وسلم: "**أَبَرُّ البِرِّ أنْ يَصِلَ الرَّجُلُ وُدَّ أبِيهِ**". رواه مسلم.

An karɓo daga Ibnu Umar Allah Ya yarda da su, ya ce: Annabi ﷺ ya ce: "Biyayyar da ta fi; ita ce mutum ya sada zumuncin wadanda mahaifinsa yake ƙauna". Muslim ne ya rawaito shi.

80. عن سالم، عن أبيه عمر رضي الله عنهما، أن رسول الله صلى الله عليه وسلم، قال: "**لَا حَسَدَ إلَّا في اثْنَتَيْنِ: رَجُلٌ آتاهُ اللَّهُ القُرْآنَ فَهو يَتْلُوهُ آناءَ اللَّيْلِ، وآناءَ النَّهارِ، ورَجُلٌ آتاهُ اللَّهُ مالًا، فَهو يُنْفِقُهُ آناءَ اللَّيْلِ، وآناءَ النَّهارِ**". متفق عليه.

An karɓo daga Salim daga Mahaifinsa, Allah Ya yarda da su, ya ce: Annabi ﷺ ya ce: "Ba hassada sai a abubuwa biyu: Mutumin da Allah Ya ba shi Ƙur'ani, kuma yake karanta shi dare da rana, da kuma mutumin da Allah Ya ba shi dukiya, yake ciyar da ita dare da rana". Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi.

81. عن جابر رضي الله عنه، عن رسول الله صلى الله عليه وسلم قال: "**لَا تَأْكُلُوا بالشِّمالِ، فإنَّ الشَّيْطانَ يَأْكُلُ بالشِّمالِ**". رواه مسلم.

An karɓo daga Jabir Allah Ya yarda da shi, daga Annabi ﷺ ya ce: "Kada ku ci da hannun hagu, haƙiƙa Shedan da hannun hagu yake ci". Muslim ne ya rawaito shi.

82. عن جابر رضي الله عنه، عن رسول الله صلى الله عليه وسلم قال: "**مَن لَقِيَ اللَّهَ لا يُشْرِكُ به شَيْئًا دَخَلَ الجَنَّةَ، ومَن لَقِيَهُ يُشْرِكُ به شَيْئًا دَخَلَ النَّارَ**". رواه مسلم.

An karɓo daga Jabir Allah Ya yarda da shi, daga Annabi ﷺ ya ce: "Wanda ya haɗu da Allah ba ya shirka da shi; zai shiga aljanna, wanda ya haɗu da shi yana haɗa shi da wani; zai shiga wuta". Muslim ne ya rawaito shi.

83. عن جابر رضي الله عنه، عن رسول الله صلى الله عليه وسلم قال: "**إِنَّ بيْنَ الرَّجُلِ وبيْنَ الشِّرْكِ والْكُفْرِ تَرْكُ الصَّلاةِ**". رواه مسلم.

An karɓo daga Jabir Allah Ya yarda da shi, daga Annabi ﷺ ya ce: "Haƙiƙa tsakanin mutum da shirka, da kafirci, shi ne barin salla". Muslim ne ya rawaito shi.

84. عن جابر رضي الله عنه، عن رسول الله صلى الله عليه وسلم قال: "**يُبْعَثُ كُلُّ عَبْدٍ عَلَى مَا مَّاتَ عَلَيْهِ**". رواه مسلم.

An karɓo daga Jabir Allah Ya yarda da shi, daga Annabi ﷺ ya ce: "Za a tashi kowanne mutum a kan abin da ya mutu a kansa". Muslim ne ya rawaito shi.

85. عن بعض أزواج النبي ﷺ عن النبي ﷺ قال : "**مَنْ أَتَى عَرَّافًا، فَسَأَلَهُ عَنْ شَيْءٍ، لَمْ تُقْبَلْ لَهُ صَلَاةٌ أَرْبَعِينَ لَيْلَةً**". رواه مسلم.

An karɓo daga wasu daga cikin matan Annabi ﷺ, Allah Ya yarda da su, daga Annabi ﷺ ya ce: "Duk wanda ya je wajen ɗan duba, ya tambaye shi wani abu; ba za a karɓi sallarsa ta kwana arba'in ba". Muslim ne ya rawaito shi.

86. عن ابن مسعود رضي الله عنه، عن رسول الله صلى الله عليه وسلم قال: "**إنَّ أشَدَّ النَّاسِ عَذابًا عِنْدَ اللهِ يومَ القِيامَةِ المُصَوِّرُونَ**". متفق عليه.

An karɓo daga Ibnu Mas'ud Allah Ya yarda da shi, daga Annabi ﷺ ya ce: "Haƙiƙa mafiya a zaba a ranar ƙiyama; su ne masu hoto". Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi.

87. عن ابن مسعود رضي الله عنه، عن رسول الله صلى الله عليه وسلم قال: **"مَن قَرَأَ بالآيَتَيْنِ مِن آخِرِ سُورَةِ البَقَرَةِ في لَيْلَةٍ كَفَتَاهُ"**. رواه البخاري.

An karɓo daga Ibnu Mas'ud Allah Ya yarda da shi, daga Annabi ﷺ ya ce: "Duk wanda ya karanta ayoyi biyu na karshen Suratul Baƙara a dare; to sun isar masa". Bukhari ne ya rawaito shi.

88. عن ثابت بن الضحاك رضي الله عنه، عن رسول الله صلى الله عليه وسلم قال: **"لَعْنُ الْمُؤْمِنِ كَقَتْلِهِ"**. متفق عليه.

An karɓo daga Sabit binud Dahhak Allah Ya yarda da shi, daga Annabi ﷺ ya ce: "Tsine wa mumini kamar kashe shi ne". Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi.

89. عن أبي ذر رضي الله عنه قال: قال النبي صلى الله عليه وسلم: **"لَا تَحْقِرَنَّ مِنَ المَعْرُوْفِ شَيْئًا وَلَوْ أَنْ تَلْقَى أَخَاكَ بِوَجْهٍ طَلِقٍ"**. رواه مسلم.

An karɓo daga Abu Zar Allah Ya yarda da shi, ya ce: Annabi ﷺ ya ce: "Kada ka raina abu mai kyau, ko da ka haɗu da ɗan'uwanka da sakakkiyar fuska ne". Muslim ne ya rawaito shi.

90. عن أبي الدرداء رضي الله عنه قال: قال النبي صلى الله عليه وسلم: **"مَا مِنْ عَبْدٍ مُسْلِمٍ يَدْعُو لأَخِيهِ بظَهْرِ الغَيْبِ، إلَّا قالَ المَلَكُ: وَلَكَ بمِثْلٍ"**. رواه مسلم.

An karɓo daga Abud Darda'i Allah Ya yarda da shi, ya ce, Annabi ﷺ ya ce: "Ba wani musulmi da zai yi wa ɗan'uwansa addu'a a bayan idonsa, face mala'iku sun ce: Kai ma Allah ya yi maka irin haka". Muslim ne ya rawaito shi.

91. عن معاوية رضي الله عنه قال: قال النبي صلى الله عليه وسلم: "**مَنْ يُرِدِ اللَّهُ بِهِ خَيْرًا؛ يُفَقِّهْهُ فِي الدِّينِ**". متفق عليه.

An karɓo daga Mu'awuya Allah Ya yarda da shi, ya ce: Annabi ﷺ ya ce: "Wanda Allah ya ke son shi da alheri; sai ya fahimtar da shi addini". Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi.

92. عن أبي سعيد الخدريّ رضي الله عنه قال: قال النبي صلى الله عليه وسلم: "**إذَا سَمِعْتُمُ النِّدَاءَ، فَقُولوا مِثْلَ ما يقولُ المُؤَذِّنُ**". متفق عليه.

An karɓo daga Abu Sa'idinil Khudri Allah Ya yarda da shi, ya ce: Annabi ﷺ ya ce: "Idan kuka ji kiran salla; to ku faɗi irin abin da ladan yake faɗi". Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi.

93. عن أبي قتادة رضي الله عنه قال: قال النبي صلى الله عليه وسلم: "ِ **ذَا دَخَلَ أحَدُكُمُ المَسْجِدَ، فَلْيَرْكَعْ رَكْعَتَيْنِ قَبْلَ أنْ يَجْلِسَ**". متفق عليه.

An karɓo daga Abu Ƙatadata Allah Ya yarda da shi, ya ce: Annabi ﷺ ya ce: "Idan ɗayanku ya shiga masallaci; to ya yi salla raka'a biyu kafin ya zauna". Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi.

94. عن أبي موسى رضي الله عنه قال: قال النبي صلى الله عليه وسلم: **"مَثَلُ الَّذِي يَذْكُرُ رَبَّهُ والَّذِي لَا يَذْكُرُ رَبَّهُ، مَثَلُ الحَيِّ والمَيِّتِ"**. رواه البخاريّ.

An karɓo daga Abu Sa'idinil Khudri Allah Ya yarda da shi, ya ce: Annabi ﷺ ya ce: "Misalin mai ambaton Ubangijinsa, da wanda ba ya amboton Ubangijinsa, kamar rayayye da macacce ne". Bukhari ne ya rawaito shi.

95. عن ابن عباس رضي الله عنهما قال: قال النبي صلى الله عليه وسلم: **"نِعْمَتانِ مَغْبُونٌ فِيهِما كَثِيرٌ مِنَ النَّاسِ: الصِّحَّةُ والفَراغُ"**. رواه البخاريّ.

An karɓo daga Ibnu Abbas Allah Ya yarda da su, ya ce: Annabi ﷺ ya ce: “Ni’immomi biyu ana bugun hancin mutane da yawa game da su: Lafiya, da kuma lokaci”. Muslim ne ya rawaito shi.

96. عن ابن عثمان بن عفان رضي الله عنه قال: قال النبي صلى الله عليه وسلم: **"خَيْرُكُمْ مَنْ تَعَلَّمَ القُرْآنَ وعَلَّمَهُ"**. رواه البخاريّ.

An karɓo daga Usman bin Affan Allah Ya yarda da shi, ya ce: Annabi ﷺ ya ce: “Mafi alherinku; shi ne wanda ya koyi Kur’ani, kuma ya koyar da shi”. Bukhari ne ya rawaito shi.

97. عن ابن عثمان بن عفان رضي الله عنه قال: قال النبي صلى الله عليه وسلم: **"مَنْ تَوَضَّأَ فأَحْسَنَ الوُضُوءَ خَرَجَتْ خَطَايَاهُ مِن جَسَدِهِ، حتَّى تَخْرُجَ مِن تَحْتِ أَظْفَارِهِ"**. رواه مسلم.

An karɓo daga Usman bin Affan Allah Ya yarda da shi, ya ce: Annabi ﷺ ya ce: "Wanda ya yi alwala, ya kuma kyautata alwalar, zunubansa zasu fita daga jikinsa, har su fuce ta ƙarƙashin faratansa". Muslim ne ya rawaito shi.

98. عن ابن عثمان بن عفان رضي الله عنه قال: قال النبي صلى الله عليه وسلم: **"مَن صَلَّى العِشَاءَ فِي جَمَاعَةٍ فكَأَنَّمَا قَامَ نِصْفَ اللَّيْلِ، وَمَن صَلَّى الصُّبْحَ فِي جَمَاعَةٍ فكَأَنَّمَا صَلَّى اللَّيْلَ كُلَّهُ"**. رواه مسلم.

An karɓo daga Usman bin Affan Allah Ya yarda da shi, ya ce: Annabi ﷺ ya ce: "Wanda ya yi sallar Isha'i a cikin jama'a; kamar ya yi tsayuwar rabin dare ne, wanda ya yi sallar Asuba a cikin jama'a; kamar wanda ya yi tsayuwar dare ne gabadayansa" Muslim ne ya rawaito shi.

99. عن أبي أيوب رضي الله عنه قال: قال النبي صلى الله عليه وسلم: **"مَن صَامَ رَمَضَانَ، ثُمَّ أَتْبَعَهُ سِتًّا مِن شَوَّالٍ، كانَ كَصِيامِ الدَّهْرِ"**. رواه مسلم.

An karɓo daga Abi Ayyubal Aansari Allah Ya yarda da shi, ya ce: Annabi ﷺ ya ce: "Wanda ya yi azumin Ramadana; kuma ya bi shi da azumi shida na Shawwal; kamar ya azumci zamani (shekara) ne". Muslim ne ya rawaito shi.

100. عن سهل بن حُنيف رضي الله عنه قال: قال النبي صلى الله عليه وسلم: **"مَن سَأَلَ اللَّهَ الشَّهادَةَ بصِدْقٍ، بَلَّغَهُ اللَّهُ مَنازِلَ الشُّهَداءِ، وإنْ ماتَ علَى فِراشِهِ"**. رواه مسلم.

An karɓo daga Sahal bin Hunaif Allah Ya yarda da shi, ya ce: Annabi ﷺ ya ce: "Duk wanda ya roƙi Allah shahada da gaske; to Allah zai kai shi matsayin shahidai, ko da kuwa ya mutu a kan shimfidarsa". Muslim ne ya rawaito shi.

**Kammalawa**:

Godiya ta tabbata ga Allah, da Ya nuna mana kammala aikin wannan littafi, a yammacin ranar Alhamis, 27 ga watan Shawwal shekata ta 1445 bayan hijira, wanda ya yi daidai da 6 ga watan Mayu, shekara ta 2024 Miladiyya.

Ina roƙon Allah da Ya karɓi wannan aiki, Ya kuma yafe mini kusakuren da suke cikinsa. Ya jiƙan iyayenmu, da malamanmu, da dukkannin musulmin da suka bi tafarkin Manzon Allah ﷺ.

Salati da aminci su ƙara tabbata ga mafi ɗaukakar Annabawa, da Manzanni, Annabinmu Muhammad ﷺ, da iyalan gidansa, da Sahabbansa bakiɗaya.